# HABBAT SAUDA'A MAGANIN DUKKAN CUTA

Daga Manzo (s.a.w) ya ce: "Babu wani cuta sai yana da magani daga Habbat Sauda'a sai dai mutuwa"

Daga Manzo (s.a.w) ya ce: "Babu wani cuta sai yana da magani daga Habbat Sauda'a sai dai mutuwa"

Haqiqar ilimi:

An yi amfani da Habbat Sauda'a - a kashen gabas ta tsakiya da ta nesa- a matsayin magani, tun da shekaru dubu biyu, kuma aka tatso sinadarin Nijillun daga man Habbat Sada'a a shekara ta 1959 ta hannun Aldakhakhaniy da abokansa.

A cikin kwayan Habbat Sauda'a akwai daskararren mai da ya kai nauyi 40% da 1,4% mai narkakke, kuma yana dauke da sinadarai goma sha biyar:aminiya, protein, calsium, karfe, sodium, da portasium ,kuma mafi mahimmancin sinadarinta shine:- siymokiniyon,daysiymkinon,saimo haidrokiyon da saimol.

Ba a fara sanin amfanin Habbat Sauda'a ba wurin karfin garkuwan jiki ba sai daga shekara 1986 bayan da Dakta Alqady da abokansa a Amirka. Sannan aka ci gaba da yin bincike daga baya a kasashen duniya da dama,a fagage daban daban game da wannan tsiron, Dakta Alqady ya tabbatar da cewa Habbat Sauda'a yana tasiri wurin qarfafa tasirin garkuwar jiki, an gano cewa yana kara qaimi jijiyoyi kusan 72% kuma ya qara nashaxin wasu garkuwoyi masu yaqi da cuta,kusan 74% kusan dukkan binciken da aka yi daga baya sun qarfafa bayanan da Alqady daga ciki:

Abin da wata jaridar garkuwan jiki ta duniya ta rubuta a bugun Agusta 1995 game da tasirin habbat sauda'a a jijiyoyi masu qara qaimin mutum daga cutuka da dama , da kuma kara qaimin jijiyoyin jini daban dabam. Da kuma abin da majallar ta buga a bugunta na satumba 2000 game da bincike goma na tasirin man habbat sauda'a ga garkuwar cutar eytomegalovirus. A lokacin da aka zavi man habbat sauda'a don maganin wannan cutar , aka gwada bangaren da ya kamu da cutar afarkon kamuwarsa, ta hanyar tantance jijiyoyi masu kashe cutar aka auna tasirin man habbat sauda'a game da shi.ita ma majallar kansa ta turai a bugunta ta Octoba 1999 ta buga wannan bayani ta hanyar gwajin kansar ciki ta veraye. Haka ita kuma mujallar binciken maganin kansa a bugunta na mayu 1998 ta bayyana cewa man habbat sauda'a yana maganin kumburi da kansa. Haka kuma majallar magani ta Isno ta buga a adadinta na Afrilu 2000 game da tasirin man Habbat Sauda'a da kwayarsa game da maganin cutuka da dama. Haka ita ma majallar tsirrai na magani ta fabrairu 1995 ta yi bayani game da binciken ta ya tabbatar ta anfanin Habbat Sauda'a game da taimakawa gudun jini da tacewarsa da sauran bincike da dama da aka gudanar.

Fuskacin mu'ujiza:

Manzo (s.a.w) ya bamu labarin cewa: Habbat Sauda'a maganin dukan cutuka ne kuma kalmar maganin sai ta zo a sigar nakira a dukkan hadisan da suka zo, kuma ya zo a sigar tabbatarwa ba korewa ba saboda haka zamu fahimci cewa habbat sauda'a magani ne na kowa ne yanki na cuta , kuma ilimi ya tabbatar da cewa garkuwar jiki shine yanki da yake

kare mutum daga mafi yawancin cutuka, wato garkuwa na asali koko wanda aka qarfafa shi da wasu abubuwa, wanda zai qara masa qarfi na yaqi da abubuwan da suke kawo ciwo. Kamar kuma yadda ya tabbata a bincike na ilimi da aka gudanar cewa Habbat sauda'a yana qara qaimin garkuwar jiki kuma yana qarfafa jijiyoyin garkuwa kusa kashi 75% a binciken da Alqady yayi.kuma sauran bincike daga baya ya qara tabbatar da haka, ta hanyar gwajegwaje da akayi ya magance tsutsan ciki da kansa da tsargiya da macijin ciki da sauransu , da kuma qara gudun jini ta hanyar kyautatashi, da kara qarfin jijiyoyi abin da zai tabbatar da cewa maganine na dukkan komai.
Ta haka zamu ga haqiqanin ilimi ya bayyana a cikin wannan hadisin abin da yake ba wani wanda zai iya gane haka balle har ya faxa ya kuma sanar da mutane tun qarni goma sha huxu da suka gabata indai banda Manzo (s.a.w) wanda yake manzo ne daga Allah . kuma Allah ya yi gaskiya da ya kira shi da cewa ( Kuma ba ya yin Magana daga son zuciyarsa.* (Maganarsa) ba ta zamo ba, face wahayi ne da ake aikawa.*) (Al-Najm 3-4)

Daga Manzo (s.a.w) ya ce: "Babu wani cuta sai yana da magani daga Habbat Sauda'a sai dai mutuwa"

Haqiqar ilimi:
An yi amfani da Habbat Sauda'a - a kashen gabas ta tsakiya da ta nesa- a matsayin magani, tun da shekaru dubu biyu, kuma aka tatso sinadarin Nijillun daga man Habbat Sada'a a shekara ta 1959 ta hannun Aldakhakhaniy da abokansa.
A cikin kwayan Habbat Sauda'a akwai daskararren mai da ya kai nauyi 40% da 1,4% mai narkakke, kuma yana dauke da sinadarai goma sha biyar:aminiya, protein, calsium, karfe, sodium, da portasium ,kuma mafi mahimmancin sinadarinta shine:- siymokiniyon,daysiymkinon,saimo haidrokiyon da saimol.
Ba a fara sanin amfanin Habbat Sauda'a ba wurin karfin garkuwan jiki ba sai daga shekara 1986 bayan da Dakta Alqady da abokansa a Amirka. Sannan aka ci gaba da yin bincike daga baya a kasashen duniya da dama,a fagage daban daban game da wannan tsiron, Dakta Alqady ya tabbatar da cewa Habbat Sauda'a yana tasiri wurin qarfafa tasirin garkuwar jiki, an gano cewa yana kara qaimi jijiyoyi kusan 72% kuma ya qara nashaxin wasu garkuwoyi masu yaqi da cuta,kusan 74% kusan dukkan binciken da aka yi daga baya sun qarfafa bayanan da Alqady daga ciki:
Abin da wata jaridar garkuwan jiki ta duniya ta rubuta a bugun Agusta 1995 game da tasirin habbat sauda'a a jijiyoyi masu qara qaimin mutum daga cutuka da dama , da kuma kara qaimin jijiyoyin jini daban dabam. Da kuma abin da majallar ta buga a bugunta na satumba 2000 game da bincike goma na tasirin man habbat sauda'a ga garkuwar cutar eytomegalovirus. A lokacin da aka zavi man habbat sauda'a don maganin wannan cutar , aka gwada bangaren da ya kamu da cutar afarkon kamuwarsa, ta hanyar tantance jijiyoyi masu kashe cutar aka auna tasirin man habbat sauda'a game da shi.ita ma majallar kansa ta turai a bugunta ta Octoba 1999 ta buga wannan bayani ta hanyar gwajin kansar ciki ta veraye. Haka ita kuma mujallar binciken maganin kansa a bugunta na mayu 1998 ta bayyana cewa man habbat sauda'a yana maganin kumburi da kansa. Haka kuma majallar magani ta Isno ta buga a adadinta na Afrilu 2000 game da tasirin man Habbat Sauda'a da kwayarsa game da maganin cutuka da dama. Haka ita ma majallar tsirrai na magani ta fabrairu 1995 ta yi bayani game da binciken ta ya tabbatar ta anfanin Habbat Sauda'a game da taimakawa gudun jini da tacewarsa da sauran bincike da dama da aka gudanar.

Fuskacin mu'ujiza:
Manzo (s.a.w) ya bamu labarin cewa: Habbat Sauda'a maganin dukan cutuka ne kuma kalmar maganin sai ta zo a sigar nakira a dukkan hadisan da suka zo, kuma ya zo a sigar tabbatarwa ba korewa ba saboda haka zamu fahimci cewa habbat sauda'a magani ne na kowa ne yanki na cuta , kuma ilimi ya tabbatar da cewa garkuwar jiki shine yanki da yake kare mutum daga mafi yawancin cutuka, wato garkuwa na asali koko wanda aka qarfafa shi da wasu abubuwa, wanda zai qara masa qarfi na yaqi da abubuwan da suke kawo ciwo. Kamar kuma yadda ya tabbata a bincike na ilimi da aka gudanar cewa Habbat sauda'a yana qara qaimin garkuwar jiki kuma yana qarfafa jijiyoyin garkuwa kusa kashi 75% a binciken da Alqady yayi.kuma sauran bincike daga baya ya qara tabbatar da haka, ta hanyar gwajegwaje da akayi ya magance tsutsan ciki da kansa da tsargiya da macijin ciki da sauransu , da kuma qara gudun jini ta hanyar kyautatashi, da kara qarfin jijiyoyi abin da zai tabbatar da cewa maganine na dukkan komai.
Ta haka zamu ga haqiqanin ilimi ya bayyana a cikin wannan hadisin abin da yake ba wani wanda zai iya gane haka balle har ya faxa ya kuma sanar da mutane tun qarni goma sha huxu da suka gabata indai banda Manzo (s.a.w) wanda yake manzo ne daga Allah . kuma Allah ya yi gaskiya da ya kira shi da cewa ( Kuma ba ya yin Magana daga son zuciyarsa.* (Maganarsa) ba ta zamo ba, face wahayi ne da ake aikawa.*) (Al-Najm 3-4)